## SŨRATUZ ZALZALA سُورَةُ الزَّلْزَلَةِ

Tana karantar da yadda mõtsin Tãshin Kiyãma yake, da bai wa mutãne sakamakon ayyukansu.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

إِذَا زُلْزِلَتِ ٱلْأَرْضُ زِلْزَالَهَا ١

*1.* Idan aka girgiza ƙasa, girgizawarta.

وَأَخْرَجَتِ ٱلْأَرْضُ أَثْقَالَهَا ٢

*2.* Kuma ƙasa ta fitar da kayanta, masu nauyi,

وَقَالَ ٱلْإِنسَٰنُ مَا لَهَا ٣

*3.* Kuma mutum ya ce "Mẽ ne ya same ta?"

يَوْمَئِذٍ تُحَدِّثُ أَخْبَارَهَا ٤

*4.* A rãnar nan, zã ta faɗi lãbãrinta,

بِأَنَّ رَبَّكَ أَوْحَىٰ لَهَا ٥

*5.* Cewa Ubangijinka Ya yi umurni zuwa gare ta.

يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْا۟ أَعْمَٰلَهُمْ ٦

*6.* A rãnar nan, mutane za su fito dabam-dabam domin a nuna musu ayyukansu.

فَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُۥ ٧

*7.* To, wanda ya aikata (wani aiki) gwargwadon nauyin zarra, na alheri, zai gan shi;

وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُۥ ٨

*8.* Kuma wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi.